# Ikon Allah



Mai tarawa Watson Goodman

Kyauta ce – Kada a sayas

# IKON ALLAH

Yaya mutum zai iya nuna ma wani ikon Allah Mahalici, ko yaya ya iya furta girman Allah wanda ikonsa ba shi da iyaka? Ba shi yiwuwa domin Allah yana da iko ba iyaka, girmansa da darajarsa sun fi tunanin mutum nisa har mu da ḳaramin tunaninmu ba mu iya fahimce shi ba.

Allah ya bayyana Kansa cikin Littafinsa, Littafi Mai Tsarki, da ya isa mu sani lalle Ikonsa ya aikata abin da mutum ya aza ba shi yiwuwa ba! Shi ya hallici duniya. Ya shimfida ta a sararin sammai, ba abin da ke riḳe ta ba sai ikon Allah kaḍai. Yana riḳa sake cika abin da ta ke bukata har wa yau ko da shi ke Shaiḍan da mutane suna ḳoḳari su hallakad da ita, ko su yi ḅarna.

Bari dai mu duba waḍansu ayoyi cikin Maganar Allah inda Ya bayyana ikonsa mara iyaka.

**Watson Goodman (1920-2002)**

The Scripture text reprinted from the Bible in Hausa by permission of United Bible Societies Africa Regional Centre, Nairobi, Kenya.

Shi ne, ta wurin ikonsa ya yi duniya, ta wurin hikimarsa ya kafa ta, ta wurin basirarsa kuma ya shimfiɗa sammai. —Irmiya 10.12

Da wa za a iya kwatanta Allah? Wanda yake zaune a kursiyi ne ya yi ta, can ƙwanƙolin duniya, gaba kuma da sararin sama, yana ganin mutane a ƙarƙas kamar'yan ƙananan ƙwari. Ya miƙa sararin sama kamar labule, kamar kuma alfarwa domin mutane su zauna ciki. Da wanene za a kwatanta Allah Mai Tsarki? Ko akwai wani mai kama da shi? Ka dubi sararin sama a bisa! Wanene ya halicci taurarin da kake gani? Shi wanda yake musu jagora kamar sojoji, ya sani ko su guda nawa ne, yana kiran dukansu, kowanne da sunansa! Ikonsa da girma yake, ba a taɓa rasa ko ɗayansu ba!
—Ishaya 40.18a, 22, 25 da 26

"Ya Ubangiji Allah, kai ne ka yi sammai da duniya ta wurin ikonka da ƙarfinka, ba abin da ya fi ƙarfinka." —Irmiya 32.17

Allah ... amma a zamanin nan na ƙarshe sai ya yi mana magana ta wurin Ɗansa, wanda ya sa magajin kome, wanda ta wurinsa ne kuma ya halicci duniya.
—Ibraniyawa 1.1a, 2

# SHAIDAN BAI DA IKO SHI HALLICI DUNIYA KO SHI SHIMFIDDA TA A SARARIN SAMMAI BA

Tun fil azal akwai Kalma, Kalman nan kuwa tare da Allah yake, Kalman nan kuwa Allah ne. Dukan abubuwa sun kasance ta gare shi ne, ba kuma abin da ya kasance na abubuwan da suka kasance, sai ta game da shi. Ɓarawo yakan zo ne kawai don sata da kisa da hallarkarwa.

—Yahaya 1.1 da 3; 10.10a

Sai ya ce musu, "Na ga Shaiɗan ya faɗo daga sama kamar walƙiya."
—Luka 10.18

Ku natsu, ku kuma zauna a faɗake. Magabcinku Iblis na zazzāgawa kamar zaki mai ruri, yana neman wanda zai lanƙwame.

—1 Bitrus 5.8

To, da ya ke mu zuriyar Allah ne, ai, bai kamata mu tsammaci Allah na kama da wata surar zinariya, ko ta azurfa, ko ta dutse ba, wadda mutum ya ƙago ta dabararsa.
—Ayyukan Manzanni 17.29

Ba na fa so ku zama abokan tarayya da aljannu.

—1 Korantiyawa 10.20b

Sai Yesu ya ƙara musu da cewa, "Ni ne Hasken duniya. Wanda ke bina ba zai yi tafiya a duhu ba, amma zai sami hasken rai."

—Yahaya 8.12

Sau ɗaya Allah ya faɗa, sau biyu na ji, cewa Allah yake da iko.
—Zabura 62.11

Allahnmu yana Sama, yana aikata yadda yake so. —Zabura 115.3

"Ni ne Allah, haka kuwa nake tutur, ba wanda zai iya tserewa daga ikona." —Ishaya 43.13a

Girma, da iko, da daraja, da nasara, da ɗaukaka duk naka ne, ya Ubangiji, gama dukan abin da ke cikin sammai da duniya naka ne. Mulki kuma naka ne, ya Ubangiji. Kai ne Maɗaukaki duka. Dukan wadata da girma daga gare ka suke, kai kake mulki da dukan iko da ƙarfi. Kai ne ke da iko ka ba mutum iko da ƙarfi.
—1 Tarihi 29.11, 12

" 'Ya Ubangiji Allah, kai ne ka fara nuna wa baranka ɗaukakarka da ikonka. Ba wani Allah a Sama ko a duniya da zai aikata ayyuka na banmamaki irin naka.' "
—Maimaitawar 3.24

"Ba wata faɗar Allah da za ta kasa cika." —Luka 1.37

" 'Kada ka kai mu wurin jaraba, amma ka cece mu daga Mugun.' " —Matiyu 6.13

Kai ne Allah wanda ke aikata al'ajabai, ka nuna ikonka cikin sauran al'umma. —Zabura 77.14

Cikin girman ɗaukakarka, ka kā da maƙiyanka, ka aika da hasalarka, ka cinye su kamar ciyawa.
—Fitowa 15.7

Ubangijinmu mai girma ne, Mai Iko Dukka, saninsa ya fi gaban aunawa. —Zabura 147.5

Amma duk da haka ya cece su, kamar yadda ya alkawarta, domin ya nuna ikonsa mai girma.
—Zabura 106.8

Sa'an nan suka yi wannan addu'a, suka ce, "Kai kaɗai ne Ubangiji, ya Ubangiji, kai ne ka yi samaniya da taurari da sararin sama. Kai ne ka yi ƙasa, da teku, da kowane abu da ke cikinsu, ka ba dukansu rai, ikokin samaniya sun rusuna suna maka sujada."
—Nehemiya 9.6

Ka yabi Ubangiji, ya raina! Ya Ubangiji Allahna, mai girma ne kai! Kana saye da ɗaukaka da daraja. —Zabura 104.1

Kowace rana zan yi maka godiya, zan yabe ka har abada abadin. Ubangiji mai girma ne, dole ne a fifita yabonsa, girmansa ya fi ƙarfin ganewa. —Zabura 145.2, 3

Suna cewa, "Mun gode maka, ya Ubangiji Allah, Maɗaukaki, wanda yake a yanzu, shi ne kuma a dā, saboda ka ɗauki ikonka mai girma, kana mulki.
—Wahyin Yahaya 11.17

Ta haka kuma za a ba ku cikakken 'yancin shiga madawwamin mulki na Ubangijinmu Mai Cetonmu Yesu Almasihu. —2 Bitrus 1.11

Ku dogara ga Ubangiji har abada. Zai kiyaye mu kullayaumin.
—Ishaya 26.4

Kafin a kafa tuddai, kafin kuma ka sa duniya ta kasance, kai Allah ne, Madawwami. Ba ka da farko, ba ka da ƙarshe. —Zabura 90.2

Amma Ubangiji shi ne Allah na gaskiya, shi Allah mai rai ne, shi Sarki ne madawwami. Saboda hasalarsa duniya ta girgiza, al'ummai ba za su iya jurewa da fushinsa ba. —Irmiya 10.10

Aka ji waɗansu muryoyi masu ƙara a Sama, suna cewa, "Mulkin duniya ya zama mulkin Ubangijinmu da na Almasihunsa, shi kuma zai yi mulki har abada abadin."
—Wahayin Yahaya 11.15b

ZA A HALLAKADDA IKON SHAIḌAN

Shi kuwa Iblis mayaudarinsu, sai da aka jefa shi tafkin wuta da kibritu, . . . za a kuma gwada musu azaba dare da rana har abada abadin. —Wahayin Yahaya 20.10

"Alamunsa da girma suke! Al'ajabansa da bantsoro suke! Sarautarsa ta har abada ce."
—Daniyel 4.3a

Da Musa ya miƙa hannunsa bisa bahar, sai Ubangiji ya sa iskar gabas mai ƙarfi ta tsaga bahar, ta tura ta baya, ta yi ta hurawa dukan dare har bahar ta bushe, ruwan kuwa ya dāre. Isra'ilawa kuwa suka bi ta tsakiyar bahar, a busasshiyar ƙasa. Ruwan ya zama musu katanga dama da hagu. Sa'an nan Ubangiji ya ce wa Musa, "Miƙa hannunka bisa bahar domin ruwa ya koma bisa kan Masarawa, da bisa karusansu, da mahayan dawakansu." Gari na wayewa sai Musa ya miƙa hannunsa bisa bahar, ruwan kuwa ya koma kamar yadda yake a dā. Da Masarawa suka yi ƙoƙarin tserewa, sai ruwan ya rufe su. Ubangiji kuwa ya hallaka su a tsakiyar bahar. Ruwan ya komo ya rufe dukan karusai, da mahayan dawakai, da dukan rundunar Fir'auna waɗanda suka bi ta cikin bahar, ba ko ɗaya da ya ragu. A wannan rana, Ubangiji ya ceci Isra'ilawa daga hannun Masarawa. Isra'ilawa kuwa suka ga gawawwakin Masarawa a bakin bahar. Isra'ilawa suka ga gawurtaccen aikin da Ubangiji ya yi gāba da Masarawa. Isra'ilawa kuwa suka ji tsoron Ubangiji, suka gaskata Ubangiji da bawansa Musa.

—Fitowa 14.21, 22, 26-28, 30, 31

# BABU WATA MU'UJIZA WADDA TA FI IKON ALLAH IYAWA

### YA BA SU RUWAN SHA

"Zan tsaya a dutsen Horeb can a gabanka. Za ka bugi dutsen, ruwa kuwa zai fito domin jama'a su sha." —Fitowa 17.6a

### YA RABA RUWAYEN TEKU DON MUTANINSA SUKA KETARA A KAN SANDARARRIYAR ƘASA.

Firistoci kuwa waɗanda ke ɗauke da akwatin alkawari na Ubangiji suka yi ta tsayawa a bisa sandararriyar ƙasa a tsakiyar Urdun har al'ummar ta gama hayewa. —Joshuwa 3.17b

### YA CIYADDA MUTANE ZAMBA SHEKARA ARBA'IN

" 'A tsakanin faɗuwar rana da almuru, za ku ci nama, da safe za ku kuma ƙoshi da abinci. Sa'an nan za ku sani, ni Ubangiji Allahnku ne.' " Da maraice makware suka zo suka rufe zangon, da safe kuma raɓa ta kewaye zangon. Sa'ad da raɓar ta kaɗe, sai ga wani abu tsaki-tsaki mai laushi, fari, kamar hazo a ƙasa. Sa'ad da Isra'ilawa suka gan shi, suka ce wa junansu, "Manna". Shekara arba'in Isra'ilawa suka yi suna cin manna, har suka kai ƙasar da ke da mutane. —Fitowa 16.12b-15a da 35a

Sai aka ɗaure su suna saye da rigunansu da wandunansu, da hulunansu, da sauran tufafinsu, aka jefa su a tanderun gagarumar wuta. Tsananin umarnin sarki ya sa aka haɓaka wutar, sai harshen wutar ya kashe waɗanda suka jefa su Shadrak, da Meshak, da Aben-nego cikin wutar. Sa'an nan mutanen nan uku, wato Shadrak, da Meshak, da Abed-nego suka faɗi a tanderun gagarumar wuta a ɗaure. Sa'an nan su hakimai, da wakilai, da muƙaddasai, da man-yan 'yan majalisa suka taru, suka ga lalle wutar ba ta yi wa jikunan mutanen nan lahani ba, gashin kawunansu bai ƙuna ba, tufafinsu ba su ci wuta ba, ko warin wuta babu a jikinsu.

—Daniyel 3.21-23 da 27

Sarki kuwa ya umarta a kawo Daniyel, a tura shi cikin kogon zakoki. Sarki kuma ya ce wa Daniyel, "Ina fata Allahn nan wanda kake bauta masa kullum zai cece ka." Sai Daniyel ya ce wa sarki, "Ran sarki ya daɗe! Allahna ya aiko mala'ikunsa ya rufe bakunan zakoki, ba su iya yi mini lahani ba, domin ban yi wa Allah laifi ba, ban kuma yi maka ba."

—Daniyel 6.16 da 21, 22

Maganata kamar wuta ce, kamar guduma mai farfashe dutse. Ni Ubangiji na faɗa.
—Irmiya 23.29

Domin Maganar Allah rayayyiya ce, mai ƙarfin aiki, ta fi kowane takobi kaifi, har tana ratsa rai da ruhu, da kuma gaɓoɓi, har ya zuwa cikin ɓargo, tana kuma iya rarrabe tunanin zuciya da manufa tata. —Ibraniyawa 4.12

Ku kuma ɗauki kwalkwalin ceto, da takobin Ruhu, wato Maganar Allah. —Afisawa 6.17

Kaƙa saurayi zai kiyaye ransa da tsarki? Sai ta wurin biyayya da umarnanka. —Zabura 119.9

Koyanzu ma ku tsarkakakku ne saboda maganar da na faɗa muku. —Yahaya 15.3

Ka tsarkake su cikin gaskiya. Maganarka ita ce gaskiya.
—Yahaya 17.17

Kuna riƙe da maganar rai kankan. —Filibiyawa 2.16a

Sai Yesu ya ce wa Yahudawan nan da suka gaskata shi, "In dai kun zauna kan maganata, hakika ku almajiraina ne. —Yahaya 8.31

Maganarka tabbatacciya ce, ya Ubangiji, a kafe take a Sama.
—Zabura 119.89

Fassarar koyarwarka takan ba da haske, takan ba da hikima ga wanda bai ƙware ba.
—Zabura 119.130

# 10 YESU KRISTI ALLAH NE CIKIN JIKIN MUTUM

Domin a cikinsa ne cikin jiki dukkan cikar allahntaka ke tabbata. —Kolosiyawa 2.9

"Ga shi, budurwa za ta yi juna biyu, ta haifi ɗa, za a kuma sa masa suna Immanuwel." (Ma'anar Immanuwel kuwa, Allah na tare da mu.) Da Yusufu ya farka daga barci, sai ya bi umarnin mala'ikan Ubangiji, ya ɗauki mata tasa, amma bai san ta ba, sai bayan ta haifi ɗanta, ya kuma sa masa suna Yesu. —Matiyu 1.23-25

Yesu kuwa ya amsa musu ya ce, "Ubana na aiki har yanzu, ni ma ina yi." Don haka Yahudawa suka ƙara nema su kashe shi, ba wai don ya keta Asabar kaɗai ba, har ma domin ya ce Allah Ubansa ne, wato yana daidaita kansa da Allah. —Yahaya 5.17, 18

Amma ga tsarkinsa na ruhu shi Ɗan Allah ne, da iko aka ayyana shi haka ta wurin tashinsa daga matattu. —Romawa 1.4

### JININ YESU KRISTI SHI JININ ALLAH NE

Ku kula da kanku, da kuma duk garken da Ruhu Mai Tsarki ya sa ku ku zama masu kula da shi, kuna kiwon Ikilisiyar Allah wadda ya sama wa kansa da jininsa. —Ayyukan Manzanni 20.28

Da kuma Yesu Almasihu . . . "Ni ne Alfa, ni ne Omega." in ji Ubangiji Allah, wanda yake a yanzu, shi ne a dā, shi ne kuma nan gaba, Maɗaukaki.

—Wahayin Yahaya 1.5a da 8

Ya tsamo mu daga mulkin duhu, ya maishe mu ga mulkin ƙaunataccen Ɗansa, wanda ta gare shi ne muka sami fansa, wato gafarar zunubanmu. Shi ne surar Allah marar ganuwa, magaji ne tun ba a halicci kome ba, don ta gare shi ne aka halicci dukkan kome, abubuwan da ke sama da abubuwan da ke ƙasa, masu ganuwa da marasa ganuwa, ko kursiyai, ko masu mulki, ko masarauta, ko masu iko, wato dukkan abubuwa an halicce su ne ta wurinsa, shi ne kuma makoma tasu.

—Kolosiyawa 1.13-16

Ka bi umarninsa, ba tare da wani aibi ko zargi ba, har ya zuwa bayyanar Ubangijinmu Yesu Almasihu, wannan kuwa makaɗaicin mamallaki abin yabo, Sarkin sarakuna, Ubangijin iyayengiji zai bayyana shi a lokacinsa. Shi ne kaɗai marar mutuwa, yake kuma zaune cikin hasken da ba ya kusatuwa. Shi kuwa ba mutumin da ya taɓa ganinsa, ko kuwa zai iya ganinsa. Girma da madawwamin mulki su tabbata gare shi. Amin, amin.

—1 Timoti 6.14-16

Wanda kuma ke dubana, yana duban wanda ya aiko ni ne.

—Yahaya 12.45

Shi ne hasken ɗaukakar Allah, ainihin kamannin zatinsa kuma, shi kuma yana riƙe da dukan abubuwa ta ikon faɗa tasa. Bayan ya tsarkake zunubanmu, sai ya zauna dama ga Maɗaukaki a can Sama.

—Ibraniyawa 1.3

Da kuma komenene girman ikonsa marar misaltuwa da yake zartarwa a gare mu, mu masu ba da gaskiya, wato zantarwar ƙarfin ikon nan nasa, wanda ya zartar ga Almasihu sa'ad da ya tashe shi daga matattu, ya kuma ba shi wurin zama a damansa a samaniya, can birbishin dukkan sarauta da iko, da ƙarfi, da mulki, birbishin kowane suna da za a sa, ba wai a duniyan nan kawai ba, har a lahira ma. Allah kuma ya sarayar da kome ƙarƙashin ikon Almasihu.

—Afisawa 1.19-22a

"Ni da Uba ɗaya muke. Amma in su nake yi, ko ba ku gaskata ni ba, to, ku gaskata ayyukan, don ku sani, ku kuma gane, Uba na cikina, ni kuma ina cikin Uba."

—Yahaya 10.30 da 38

Ya kuma ba shi ikon zartar da hukunci, saboda shi Ɗan Mutum ne.

—Yahaya 5.27

### SHI ḌAYA NE CIKIN UKU

Ruhu kuma shi ne mai ba da shaida, domin Ruhun shi ne gaskiya. —1 Yahaya 5.7

Sai Bitrus ya ce, "Kai, Hananiya, ta ƙaƙa Shaiɗan ya cika zuciyarka, har ka yi wa Ruhu Mai Tsarki ƙarya, ka kuma ɓoye wani abu daga cikin kuɗin gonar? Kafin ka sayar, ba taka ba ce? Bayan ka sayar kuma, kuɗin ba halalinka ba ne? Ta ƙaƙa ka riya wannan aiki a zuciyarka? Ai, ba mutum ka yi wa ƙarya ba, Allah ka yi wa." Da jin wannan magana Hananiya ya faɗi ya mutu. Duk waɗanda suka ji kuwa, matsanancin tsoro ya kama su.

—Ayyukan Manzanni 5.3-5

### YA KAN CIKA ZUKATAN MASU BADA GASKIYA.

Bayan sun yi addu'a, wurin da suke tattare ya raurawa. Sai duk aka cika su da Ruhu Mai Tsarki, suka yi ta faɗar maganar Allah gabagaɗi. —Ayyukan Manzanni 4.31

### YA KAN SA ḲAMNAR ALLAH A ZUKUATAN MASU BADA GASKIYA

Ita sa zuciyan nan kuwa ba ta sāce iska faufau, domin Allah ya kwarara ƙauna tasa a zukatanmu, ta Ruhu Mai Tsarki da aka ba mu.

—Romawa 5.5

Saboda haka yana da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto, tun da ya ke kullum a raye yake saboda yi musu addu'a. —Ibraniyawa 7.25

Ga wanda ke da iko ya tsare ku daga faɗuwa, ya kuma miƙa ku marasa aibi a gaban ɗaukakarsa da matuƙar farin ciki. —Yahuza 24

Na san wanda na gaskata da shi, na kuma tabbata yana da iko ya kiyaye abin da na danƙa masa, har ya zuwa waccan rana.
—2 Timoti 1.12b

Allah kuwa na da iko ya ba ku fiye da bukatarku, domin kullum ku wadata da kome ta kowace hanya, kuna ta bayarwa hannu sake saboda kowane irin kyakkyawan aiki. —2 Korantiyawa 9.8

Allah yana da iko ya halitta wa Ibrahim 'ya'ya da duwatsun nan.
—Luka 3.8b

Ibrahim . . . ba kuwa wata rashin bangaskiyar da ta sa shi shakkar cikar alkawarin Allah, sai ma ƙara ƙarfafa ga bangaskiya tasa ya yi, yana ɗaukaka Allah, yana haƙƙaƙewa, cewa Allah na da ikon yin abin da ya yi alkawari. —Romawa 4.16c da 20, 21

Da ikon nan nasa na sarayar da dukkan abubuwa gare shi.
—Filibiyawa 3.21b

Yanzu ni, Nebukadnezzar, ina yabon Sarkin Samaniya, ina ɗaukaka shi, ina kuma girmama shi saboda dukan ayyukansa daidai ne, al'amuransa kuma gaskiya ne. Yakan ƙasƙantar da masu girmankai.''
—Daniyel 4.37

Idan haka ne, Allahnmu wanda muke bauta wa, yana da iko ya cece mu daga tanderun gagarumar wuta, zai kuwa kuɓutar da mu daga hannunka, ya sarki. Nebukadnezzar fa ya matso kusa da ƙofar tanderun gagarumar wuta, ya ce, ''Shadrak, da Meshak, da Abednego, bayin Allah Maɗaukaki, ku fito, ku zo nan!'' Suka ga lalle wutar ba ta yi wa jikunan mutanen nan lahani ba, gashin kawunansu bai ƙuna ba, tufafinsu ba su ci wuta ba, ko warin wuta babu a jikinsu.
—Daniyel 3.17 da 26a, 27b

Tun da ya ke shi ma ya sha wuya, sa'ad da aka gwada shi, ashe, zai taimaki waɗanda ake wa gwaji.
—Ibraniyawa 2.18

### IKO BISA MUTUWA

Ya amince cewa ko daga matattu Allah yana da iko ya ta da mutum.
—Ibraniyawa 11.19a

Da kuma yadda tun kana ɗan ƙaramin yaro ka san Littattafai masu tsarki, waɗanda suke koya maka hanyar samun ceto ta dalilin bangaskiya ga Almasihu Yesu.
—2 Timoti 3.15

Kai wanene har da za ka ga laifin baran wani? Ko dai ya tsaya ko ya faɗi, ai, ruwan maigidansa ne. Za a ma tsai da shi, domin Ubangiji na da ikon tsai da shi.
—Romawa 14:4

Ɗaukaka tă tabbata ga wannan da ke da ikon aikatawa fiye da dukkan abin da za mu roƙa, ko za mu zata nesa, wato aikatawa ta ƙarfin ikonsa da ke aiki a zuciyarmu. Ɗaukaka tă tabbata a gare shi a ikilisiya ta wurin Almasihu Yesu, har ya zuwa dukkan zamanai har abada abadin. Amin.
—Afisawa 3.20, 21

To, yanzu na danƙa ku ga Ubangiji, maganar alherinsa kuma tă kiyaye ku, wadda ita ke da ikon inganta ku, ta kuma ba ku gādo.
—Ayyukan Manzanni 20.32a

To, ina tambaya. Wato Allah ya juya wa jama'a tasa baya ke nan? A'a, ko kusa! Ai, ni ma kaina Ba'isra'ile ne, zuriyar Ibrahim, na kabilar Biliyaminu. Ko su ma, in dai ba su nace wa rashin bangaskiyarsu ba, sai a ɗaura aure da su, domin Allah na da ikon sāke mai da su.
—Romawa 11.1 da 23

**Idan kana yin lissafin zunubanmu, wa zai kuɓuta daga hukunci? Amma kakan gafarta mana, domin mu zama masu tsoronka.**
—Zabura 130.3, 4

**In jama'ata waɗanda ake kiransu da sunana za su yi tawali'u, su yi addu'a, su nemi fuskata, su juyo su bar mugayen ayyukansu, sa'an nan sai in ji su daga Sama, in gafarta zunubansu, in kuma warkar da ƙasarsu.** —2 Tarihi 7.14

**Wanne ya fi sauƙi, a ce wa shanyayyen, 'An gafarta maka zunubanka', ko kuwa a ce, 'Tashi ka ɗauki shimfiɗarka ka yi tafiya'? Amma don ku sakankance Ɗan Mutum na da ikon gafarta zunubi a duniya" —sai ya ce wa shanyayyen— "Na ce maka, tashi, ka ɗauki shimfiɗarka ka tafi gida." Sai ya tashi nan da nan, ya ɗauki shimfiɗarsa, ya fita a gaban idon kowa, har suka yi mamaki duka, suka ɗaukaka Allah suna cewa, "Ba mu taɓa ganin irin haka ba."**
—Markus 2.9-12

**Kowa ya kushe wa Ɗan Mutum, ā gafarta masa, amma wanda ya saɓi Ruhu Mai Tsarki, ba za a gafarta masa ba.** —Luka 12.10

**Kamar yadda Ubangiji ya yafe muku, ku kuma ku yafe.**
—Kolosiyawa 3.13b

Saboda haka, duk wanda ke na Almasihu, sabuwar halitta ne, tsohon al'amari duk ya shuɗe, ga shi, kome ya zama sabo.
—2 Korantiyawa 5.17

Wanda kuwa ke raye, yake kuma gaskatawa da ni, ba zai mutu ba har abada. Kin gaskata wannan?''
—Yahaya 11.26

Da ya kai ga kammala, sai ya zama tushen madawwamin ceto ga dukkan waɗanda suke masa biyayya.
—Ibraniyawa 5.9

Wato kamar yadda mallakar zunubi mutuwa ce, haka mallakar Allah ta alheri adalci ce, da ke bi da mu zuwa rai madawwami ta wurin Yesu Almasihu Ubangijinmu.
—Romawa 5.21

Wadda yanzu aka bayyana, ta bayyanar Mai Cetonmu Almasihu Yesu, wanda ya shafe mutuwa, ya kuma bayyana rai da rashin mutuwa, ta bishara.
—2 Timoti 1.10

Wato muddin muna raye, kullum zaman mutuwa muke yi saboda Yesu, domin a bayyana ran Yesu ta jikin nan namu mai mutuwa.
—2 Korantiyawa 4.11

Ɓarawo yakan zo ne kawai don sata da kisa da hallakarwa. Ni kuwa na zo ne domin su sami rai, . . . a yalwace.
—Yahaya 10.10

# IKON YESU KRISTI SHI WARKADDA JIKIN MUTUM



Wata rana yana koyarwa, waɗansu Farisiyawa kuwa da masanan Attaura da suka fito daga kowane gari na ƙasar Galili, da na ƙasar Yahudiya, daga kuma Urushalima, suna nan zaune. Ikon Ubangiji na warkarwa kuwa na nan. —Luka 5.17

Sai ga wata mace wadda ta shekara goma sha biyu tana zub da jini, ta kuma ɓad da duk abin hannunta wajen masu magani, ba wanda ya iya warkar da ita. Ta raɓo ta bayansa, ta taɓa gezar mayafinsa. Nan take zubar jininta ta tsaya. —Luka 8.43, 44

Duk inda ya shiga kuma, birni ko ƙauye ko karkara, sukan kwantar da marasa lafiya a bakin kasuwa, su roƙe shi su taɓa ko da gezar mayafinsa ma. Iyakar waɗanda suka taɓa shi kuwa suka warke. —Markus 6.56

Da maraice ya yi, sai suka kakkawo masa masu aljannu da yawa. Da magana kawai ya fitar da aljannun, ya kuma warkar da dukan marasa lafiya. Wannan kuwa domin a cika faɗar Annabi Ishaya ne cewa, "Da kansa ya ɗebe rashin lafiyarmu, ya ɗauke cuce-cucenmu." —Matiyu 8.16, 17

# YANA DA IKON WARKADDA KOWACE IRIN CUTA DA RASHIN LAFIYA

Sai Yesu ya miƙa hannu, ya taɓa shi, ya ce, "Na yarda, ka tsarkaka." Nan take kuturtarsa ta warke. —Matiyu 8.3

Sai ya ɗora mata hannu, nan take ta miƙe, ta kuma ɗaukaka Allah. —Luka 13.13

Nan take Yesu ya warkar da mutane da yawa daga rashin lafiyarsu da cuce-cucensu da kuma baƙaƙen aljannu. Makafi da yawa kuma ya yi musu baiwar gani. —Luka 7.21

Yana shiga wani ƙauye ke nan, sai waɗansu kutare maza guda goma suka tarye shi, suna tsaye daga nesa. Da ya gan su, ya ce musu, "Ku je wurin firistoci su gan ku." Suna tafiya ke nan, sai suka tsarkaka. —Luka 17.12 da 14

Da Yesu ya shiga gidan Bitrus, sai ya ga surukar Bitrus na kwance da zazzaɓi. Sai ya taɓa hannunta, zazzaɓin ya sake ta, ta kuma tashi ta yi masa hidima. —Matiyu 8. 14, 15

Sai ɗayansu ya kai wa bawan babban firist sara, ya ɗauke masa kunnensa na dama. Yesu ya amsa ya ce, "Ku ƙyale su haka." Sai ya taɓa kunnen bawan, ya warkar da shi. —Luka 22.50, 51

# YANA DA IKON WARKADDA KOWACE IRIN CUTA DA RASHIN LAFIYA

Da ya shiga wani gida sai makafin suka zo gare shi. Yesu ya ce musu, "Kun gaskata ina da ikon yin haka?" Sai suka ce masa, "I, ya Ubangiji!" Sa'an nan ya taɓa idanunsu, ya ce, "Yǎ zamar muku gwargwadon bangaskiyarku." Sai idanunsu suka buɗe.

—Matiyu 9.28-30a

Sa'an nan ya ce wa mutumin, "Miƙo hannunka." Ya miƙa. Sai ya koma lafiyayye kamar ɗayan.

—Matiyu 12.13

Yana shiga Kafarnahum ke nan, sai wani jarumi ya zo gunsa ya roƙe shi, ya ce, "Ya Ubangiji, yarona na kwance a gida, ya zama shanyayye, yana shan azaba ƙwarai." Yesu ya ce masa, "Zan zo in warkar da shi." Sai Yesu ya ce wa jarumin ɗin, "Je ka, ya zamar maka gwargwadon bangaskiyar da ka yi." Nan take yaronsa ya warke.

—Matiyu 8.5-7 da 13

A nan kuwa akwai wani mutum da ya shekara talatin da takwas da rashin lafiya. Sai Yesu ya ce masa, "Tashi, ka ɗauki shimfiɗarka, ka yi tafiya!" Nan take mutumin ya warke, ya ɗauki shimfiɗarsa ya yi tafiya. Ran nan kuwa Asabar ce.

—Yahaya 5.5 da 8, 9

# BABU WANI IRIN CIWO DA YA GAGGARA GARESHI

In waninku na rashin lafiya, to, sai ya kira dattawan ikilisiya. Addu'ar bangaskiya kuwa za ta warkar da marar lafiya, Ubangiji kuma zai tashe shi.
—Yakubu 5.14a, 15a

Sai ya zazzaga duk ƙasar Galili, yana koyarwa a majami'unsu, yana shelar bisharar Mulkin Allah, yana kuma warkar da kowace cuta da rashin lafiya na mutane.
—Matiyu 4.23

A kuma warkar da cuce-cucensu. Waɗanda kuma baƙaƙen aljannu ke wahalshe su, aka warkar da su. Duk taron suka nema su taɓa shi, domin iko na fitowa daga gare shi, ya kuwa warkar da su duka. —Luka 6.17b-19

Suka roƙe shi su taɓa ko da gezar mayafinsa ma, iyakar waɗanda suka taɓa kuwa suka warke.
—Matiyu 14.36

Taro masu yawan gaske suka zo wurinsa, suka zazzo da guragu, da masu dungu, da makafi, da bebaye, da kuma waɗansu da yawa, suka ajiye su a gabansa, ya kuwa warkar da su. —Matiyu 15.30

Taro mai yawan gaske suka bi shi, ya kuwa warkar da su a can.
—Matiyu 19.2

Sai Yesu ya tsawata masa, aljanin kuma ya rabu da shi. Nan take yaron ya warke.

—Matiyu 17.18

Aljannu kuma suka fita daga mutane da yawa, suna ihu suna cewa, "Kai Ɗan Allah ne!" Amma ya tsawata musu, ya hana su magana, don sun sani shi ne Almasihu.

—Luka 4.41

Da ya isa wancan hayi a ƙasar Garasinawa, mutum biyu masu aljannu suka fito daga makabarta suka tarye shi. Don kuwa su abin tsoro ne ƙwarai, har ba mai iya bi ta wannan hanya. Sai suka ƙwala ihu suka ce, "Ina ruwanka da mu, kai Ɗan Allah? Ka zo nan ne ka yi mana azaba tun kafin lokaci ya yi?" Nesa kuma kaɗan akwai wani babban garken alade na kiwo. Sai aljannun suka roƙe shi, suka ce, "In ka fitar da mu, tura mu cikin garken aladen nan." Ya ce musu, "To, ku je."

—Matiyu 8.28-32a

Sai aka kawo masa wani beben makaho mai aljan, ya kuwa warkar da shi, har beben ya yi magana, ya kuma gani.

—Matiyu 12.22

Sai ya kira sha biyun nan, ya fara aikensu biyu-biyu, ya kuma ba su iko a kan baƙaƙen aljannu.

—Markus 6.7

Haka fa, suka fita, suna wa'azi mutane su tuba. Suka fitar da aljannu da yawa.—Markus 6.12, 13a

Da Ubangiji ya gan ta, ya ji tausayinta, ya kuma ce mata, "Daina kuka." Sa'an nan ya matso, ya taɓa makarar, masu ɗauka kuma suka tsaya cik. Sai Yesu ya ce, "Samari, na ce maka ka tashi." Mamacin ya tashi zaune, ya fara magana. Yesu kuwa ya ba da shi ga uwa tasa. —Luka 7.13-15

Yesu ya ce mata, "Dan'uwanki zai tashi." Marta ta ce masa, "Na sani zai tashi a tashin matattu a ranar ƙarshe." Yesu ya ce mata, "Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu." Da ya faɗi haka ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce. "Li'a zaru, fito!" Sai mamacin ya fito, ƙafa da hannu a ɗaure da abin likkafani, fuska tasa kuma a naɗe da mayani. Yesu ya ce musu, "Ku kwance masa, ya tafi." —Yahaya 11.23-25 da 43, 44

Yana cikin magana, sai ga wani ya zo daga gidan shugaban majami'ar, ya ce, "Ai, 'yarka ta rasu. Kada ka ƙara wahalar da Malamin." Shi kuwa da ya kama hannunta, ya ta da murya ya ce, "Yarinya, ki tashi." Ruhunta kuwa ya dawo, nan take ta tashi. Sai ya yi umarni a ba ta abinci. Iyayenta suka yi mamaki.

—Luka 8.49 da 54, 55-56a

# ALKAWALIN ALLAH BATUN TASHIN MATATTU

"Lalle hakika, ina gaya muku, lokaci na zuwa, har ma ya yi, da matattu za su ji muryar Ɗan Allah, masu ji kuwa su rayu."

—Yahaya 5.25

Gama nufin Ubana, shi ne duk wanda ke duban Ɗan, yake kuma gaskatawa da shi, yă sami rai madawwami, ni kuma zan tashe shi a ranar ƙarshe." —Yahaya 6.40

Kada ku yi mamakin wannan, domin lokaci na zuwa da duk waɗanda ke kaburbura za su ji murya tasa, su kuma fito.

—Yahaya 5.28, 29a

Ina sa zuciya ga Allah, yadda su waɗannan ma suke sawa, wato za a ta da matattu, masu adalci da marasa adalci duka.

—Ayyukan Manzanni 24.15

Mun sani shi wannan da ya ta da Ubangiji Yesu daga matattu, mu ma zai tashe mu albarkacin Yesu, yă kuma kawo mu gabansa tare da ku. —2 Korantiyawa 4.14

Domin Ubangiji kansa ma zai sauko daga Sama da kira mai ƙarfi, da muryar babban mala'ika, da kuma busar ƙahon Allah. Waɗanda suka mutu suna na Almasihu, su ne za su fara tashi.

—1 Tasalonikawa 4.16

Sai Yesu ya matso, ya ce musu, "An mallaka mini dukkan iko a Sama da ƙasa." —Matiyu 28.18

Gama tun daga halittar duniya al'amuran Allah marasa gănuwa, wato ikonsa madawwami, da allahntakarsa, sun fahimtu sarai, ta hanyar abubuwan da aka halitta kuma ake gane su. Saboda haka mutane sun rasa hanzari.
—Romowa 1.20

Wanda ya tafi Sama, yake dama ga Allah kuma, mala'iku da manyan mala'iku da masu iko suna binsa. —1 Bitrus 3.22

"Mai zuwa daga Sama na sama da kowa. Wanda ke na ƙasa asalinsa kuwa na ƙasa ne, maganar ƙasa kuma yake yi. Mai zuwan nan daga Sama na sama da kowa." —Yahaya 3.31

" 'Ga maganar Mai Tsarkin nan, mai gaskiya, wanda ke da mabuɗin Dawuda, wanda in ya buɗe, ba mai rufewa, in kuma ya rufe, ba mai buɗewa.' "
—Wahayin Yahaya 3.7b

Allah da ikonsa yā yi mana baiwa da dukan abubuwan da suka wajaba ga rayuwa da kuma binsa, ta sanin wanda ya kira mu ga samun ɗaukakarsa da fifikonsa. —2 Bitrus 1.3

"Duk da haka, don kada mu ba su haushi, ka je teku ka yi fatsa, kifin da ka fara kamawa kuwa shi za ka ɗauka. In ka buɗe bakinsa za ka sami shekel guda a ciki. To, sai ka ɗauki shekel ɗin nan ka kai musu, wato nawa da naka."
—Matiyu 17.27

Domin ya san zuciyar kowa, ba kuma sai wani ya shaidi mutum a wurinsa ba, domin shi kansa ya san abin da ke zuciyar 'yan adam.
—Yahaya 2.25

A wannan rana Allah zai yi wa 'yan adam shari'a a kan asiransu, ta wurin Yesu Almasihu, bisa ga bishara da nake wa'azinta.
—Romawa 2.16

### YANA DA IKO YA CIYADDA MUTANE DUBU BIYAR

Sai suka ce masa, "Ai, gurasa biyar da kifi biyu kawai muke da shi a nan." Sai ya ce, "Ku kawo mini su." Sa'an nan ya umarci taron su zazzauna a ɗanyar ciyawa. Da ya ɗauki gurasa biyar ɗin da kifi biyun, sai ya ɗaga kai sama, ya yi wa Allah godiya, ya gutsuttsura gurasar, ya yi ta ba almajiransa, almajiran kuma suna bai wa jama'a. Duka kuwa suka ci suka ƙoshi, har suka kwashe ragowar gutsattsarin, cike da kwando goma sha biyu. Waɗanda suka ci kuwa misalin maza dubu biyar ne.
—Matiyu 14.17-21a

### YANA DA IKON TAKA RUWAN TEKU

Wajen ƙarfe uku na dare sai Yesu ya nufo su, yana tafe a kan ruwan tekun. —Matiyu 14.25

### YANA DA IKON HANA RUWAN SAMA

Suna da ikon hana ruwan sama, don kada a yi ruwa duk kwanakin da suke yin annabci, suna kuma da iko a kan ruwa, su mai da shi jini, sun kuma ɗora wa duniya kowane irin bala'i, duk lokacin da suke so. —Wahayin Yahaya 11.6

### YANA DA IKON KWANTADDA HADIRI

Ya ce musu, "Don me kuka firgita haka, ya ku masu ƙarancin bangaskiya?" Sa'an nan ya tashi, ya tsawata wa iskar da ruwan. Sai wurin duk ya yi tsit. —Matiyu 8.26

### YANA DA IKON SHIGA ƊAKI ƘOFOFFI NA KULLE

Bayan kwana takwas har wa yau almajiransa na cikin gidan, Toma ma na nan tare da su, ƙofofi na kulle, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsaka." —Yahaya 20.26a

### YANA DA IKON RIƘE HALLITARSA DUKA

Dukkan abubuwa an halicce su ne ta wurinsa, shi ne kuma makoma tasu. Shi ne gaba da dukkan abubuwa, dukkan abubuwa kuma shi ne ke riƙe da su.
—Kolosiyawa 1.16b-17

Mun sani tun da ya ke an ta da Almasihu daga matattu, ba zai sāke mutuwa ba ke nan, mutuwa ba ta da sauran wani iko a kansa.
—Romawa 6.9

In kuwa Ruhun wannan da ya ta da Yesu daga matattu na zaune a zuciyarku, to, shi da ya ta da Almasihu Yesu daga matattu zai kuma raya jikin nan naku mai mutuwa, ta Ruhunsa da ke zaune a zuciyarku. —Romawa 8.11

Ku yabi Allah da babbar murya ta farin ciki, ya jama'a duka! Ku raira waƙar darajar sunansa, ku yabe shi da ɗaukaka! Ku faɗa wa Allah cewa, "Al'amuran da kake aikatawa suna da banmamaki ƙwarai! Ikonka yana da girma ƙwarai, har maƙiyanka sukan durƙusa a gabanka don tsoro. Duk wanda yake a duniya, yana yi maka sujada, yana raira maka waƙar yabbai, yana raira yabbai ga sunanka." —Zabura 66.1-4

IKO CIKIN MULKINSA

Domin Mulkin Allah ba ga maganar baka yake ba, sai dai ga ƙarfi. —1 Korantiyawa 4.20

"Za su yaƙi Ɗan Ragon, Ɗan Ragon kuwa zai ci su, . . . domin shi ne Ubangijin iyayengiji."
—Wahayin Yahaya 17.14a

### YANA DA IKO KAN DUKAN 'YAN ADAM

Tun da ka ba shi iko a kan dukkan 'yan adam, yă ba da rai madawwami ga duk waɗanda ka ba shi. —Yahaya 17.2

### ḲASA TA YI GIRGIZA SA'ANDA YA MUTU

Sai Yesu ya sāke ɗaga murya da ƙarfi, sa'an nan ya săki ransa. . . . Kasa ta yi girgiza. —Matiyu 27.50, 51b

### YANA DA IKON TA DA KANSA DAGA MATATTU

Domin wannan Uba ke ƙaunata, domin ina ba da raina in ɗauko shi kuma. Ba mai karɓe mini rai, don kaina nake ba da shi. Ina da ikon ba da shi, ina da ikon ɗauko shi kuma. Na karɓo wannan umarni ne daga wurin Ubana." —Yahaya 10.17, 18

### YANA DA IKON BAYYANA DARAJAR SAMA

Sai kamanninsa ya sāke a gabansu, fuska tasa ta yi annuri kamar hasken rana, tufafinsa kuma suka yi fari fat suna haske. —Matiyu 17.2

### YANA DA IKON DAWO DUNIYA CIKIN DARAJA

Sai Yesu ya ce masa, "Yadda ka faɗa. Ina kuwa gaya muku nan gaba za ku ga Ɗan Mutum zaune dama da Mai Iko, yana kuma zuwa kan gajimare." —Matiyu 26.64

### YANA DA IKON GAFARTA ZUNUBAI

Amma domin ku sakankance Ɗan Mutum na da ikon gafarta zunubi a duniya" —sai ya ce wa shanyayyen— "Tashi, ka ɗauki shimfiɗarka ka tafi gida."

—Matiyu 9.6

### YANA DA IKON BADA RAI MADAWWAMI

Tumakin nan nawa sukan saurari muryata, na san su, suna kuma bina. Ina ba su rai madawwami.

—Yahaya 10.27, 28a

### YANA DA IKON CECI KOWA

A kuma yi wa dukan al'ummai wa'azi su tuba, a gafarta musu zunubansu saboda sunansa. Za a kuwa fara daga Urushalima.

—Luka 24.47

Waɗanda Ruhu kuma ya tsarkake, domin su yi wa Yesu Almasihu biyayya, su kuma tsarkaka da jininsa.

—1 Bitrus 1.2b

### YANA DA IKON BADA NASARA GA KOWA

Ubangiji zai cece ni daga kowane mugun abu, ya kuma kiyaye ni, ya kai ni Mulkinsa na Sama.

—2 Timoti 4.18a

### YANA DA IKON RIƘE MUTUM CIKIN BANGASKIYARSA

Kada bangaskiyarku ta dogara ga hikimar mutane, sai dai da ƙarfin Allah.

—1 Korantiyawa 2.5

Saboda haka ne kuma Allah ya ɗaukaka shi mafificiyar ɗaukaka, ya kuma yi masa baiwa da sunan nan da ke birbishin kowane suna, domin dai kowace gwiwa sai ta rusuna wa sunan nan na Yesu, a Sama da ƙasa. —Filibiyawa 2.9, 10a

Amma an rubuta waɗannan ne, domin ku ba da gaskiya Yesu shi ne Almasihu, Ɗan Allah, ta gaskatawa kuma ku sami rai a cikin sunansa. —Yahaya 20.31

"Malam, mun ga wani na fitar da aljannu da sunanka, mun kuwa hana shi, domin ba ya binmu." Amma Yesu ya ce, "Kada ku hana shi. Ai, ba wanda zai yi wata mu'ujiza da sunana, sa'an nan nan da nan ya kushe mini.
—Markus 9.38b, 39

Duk abin da kuka roƙa da sunana kuma zan yi, domin a ɗaukaka Uban ta wurin Ɗan. Kome kuke roƙa da sunana, zan yi shi."
—Yahaya 14.13, 14

Amma Bitrus ya ce, "Kuɗi kam ba ni da su, amma abin da nake da shi, shi zan ba ka. Da sunan Yesu Almasihu Banazare, yi tafiya." Sai Bitrus ya kama hannunsa na dama, ya tashe shi. Nan take ƙafafunsa da wuyan sawunsa suka yi ƙarfi. —Ayyukan Manzanni 3.6, 7

Ta gare shi ne muka sami fansa albarkacin jininsa, wato yafewar laifofinmu, bisa ga yalwar alherin Allah. —Afisawa 1.7

"Koƙon nan sabon alkawari ne, da aka tabbatar da jinina da za a bayar dominku." —Luka 22.20b

Sun kuwa yi nasara da shi albarkacin jinin Ɗan Ragon nan, da kuma albarkacin maganar da suka shaida.—Wahayin Yahaya 12.11a

Allah mai zartar da salama, wanda ya ta da Ubangijinmu Yesu, Makiyayin tumaki Mai Girma, daga matattu, albarkacin jinin nan na tabbatar madawwamin alkawari, yă kammala ku da kowane irin kyakkyawan abu domin ku aikata nufinsa, ya kuma aikata a cikinmu abin da ke faranta masa rai ta wurin Yesu Almasihu. Ɗaukaka tă tabbata a gare shi har abada abadin. Amin, amin. —Ibraniyawa 13.20, 21

"Su ne waɗanda suka fito daga matsananciyar wahala, sun wanke rigunansu, suka mai da su farare da jinin Ɗan Ragon nan." —Wahayin Yahaya 7.14b

In kuwa muna zaune a haske kamar yadda shi yake cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi. —1 Yahaya 1.7

Suna cewa da murya mai ƙarfi, "Macancanci ne Ɗan Rago nan da aka yanka yǎ sami iko, da wadata, da hikima, da ƙarfi, da girma, da ɗaukaka, da yabo!"
—Wahayin Yahaya 5.12

Sauran al'umma za su ji tsoron Ubangiji, dukan sarakunan duniya za su ji tsoron ikonsa. Don waɗanda ba a haife su ba tukuna, su ma su yabe shi.
—Zabura 102.15 da 18b

Amma ku kabila ce zaɓaɓɓiya, ƙungiyar firistocin babban Sarki, tsattsarkar al'umma, jama'ar mallakar Allah, domin ku sanar da mafifitan al'amuran wannan da ya kirawo ku daga cikin duhu, kuka shiga maɗaukakin haskensa.
—1 Bitrus 2.9

Ku yabi Ubangiji, shi da yake mulki a Sihiyona! Ku faɗa wa kowace al'umma abin da ya yi!
—Zabura 9.11

"Ku yabe shi, ku bayin Ubangiji!" Da ma dukan mutane su yabe ka, ya Allah, da ma dukan mutane su yabe ka! Kasa ta ba da amfaninta, Allah, wanda yake Allahnmu ne, ya sa mana albarka. Allah ya sa mana albarka, da ma dukan jama'a ko'ina su girmama shi.
—Zabura 22.23a; 67.5-7

"Malam, wane aiki nagari ne da lalle zan yi in sami rai madawwami?" Sai ya ce masa, in kuwa kana so ka sami wannan rai, to, ka kiyaye umarnan nan." Sai ya ce masa, "Waɗanne?" Yesu ya ce, "Kada ka yi kisankai. Kada ka yi zina. Kada ka yi sata. Kada ka yi shaidar zur. Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka, ka kuma ƙaunaci ɗan'uwanka kamar kanka." Saurayin ya ce masa, "Ai, duk na kiyaye waɗannan, me kuma ya rage mini?" Yesu ya ce masa, "In kana so ka zama kammalalle, sai ka je ka sayar da duk mallakarka, ka bai wa gajiyayyu, ka sami wadata a Sama. Sa'an nan ka zo ka bi ni." —Matiyu 19.16b, 17a da 17c-21

### TUBA, GASKANTA, KARƁA

Yesu ya shigo ƙasar Galili, yana yin bisharar Allah, yana cewa, "Lokaci ya yi, Mulkin Allah ya kusato. Ku tuba, ku gaskata da bishara." —Markus 1.14b, 15

Dā yana duniya, duniyar ma ta wurinsa ta kasance, duk da haka duniya ba ta san shi ba. Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah. —Yahaya 1.10 da 12

# YESU KRISTI SHI NE HANYA, GASKIYA, RAI

Domin Shari'a ta hannun Musa aka ba da ita, alheri da gaskiya kuwa ta wurin Yesu Almasihu suka kasance. —Yahaya 1.17

Yesu ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina." —Yahaya 14.6

Wanene maƙaryacin nan, in ba wanda ya mūsa Yesu shi ne Almasihu ba? Irin wannan shi ne magabcin Almasihu, shi wanda ke ƙin Uban da Ɗan. —1 Yahaya 2.22

"Ku shiga ta ƙunƙuntar ƙofa, gama ƙofa zuwa halaka faffaɗa ce, hanyarta mai sauƙin bi ce, masu shiga ta cikinta suna da yawa. Domin kuwa ƙofar zuwa rai ƙunƙunta ce, hanyarta mai wuyar bi ce, masu samunta kuwa kaɗan ne." —Matiyu 7.13, 14

Shi ne tushen rai, wannan rai kuwa shi ne hasken mutane. —Yahaya 1.4

Yadda Uba kansa yake tushen rai, haka ya sa Ɗan ya zama tushen rai. —Yahaya 5.26

"Ni ne Gurasan rai da ya sauko daga Sama. Kowa ya ci Gurasan nan, zai rayu har abada." —Yahaya 6.51a

"Duk mai gaskatawa da ni, kamar yadda Nassi ya ce, 'Daga zuciyarsa ne kogunan ruwan rai za su gudana.' " —Yahaya 7.38

Domin Almasihu bai shiga wani wuri tsattsarka da mutum ya yi ba, . . . Sama kanta ya shiga, domin yǎ bayyana a gaban zatin Allah a yanzu saboda mu. Ba kuwa domin ya riƙa miƙa kansa hadaya a kai a kai ba ne, kamar yadda babban firist ke shiga Wuri Mafi Tsarki a kowace shekara da jinin da ba nasa ba ne. In da haka ne, ashe, da sai lalle ya yi ta shan wuya a kai a kai ke nan, tun daga farkon duniya. Amma yanzu ya bayyana sau ɗaya tak a ƙarshen zamanai, domin ya kawar da zunubi ta wurin miƙa kansa hadaya. Tun da ya ke an ƙaddara wa ɗan adam ya mutu sau ɗaya ne, bayan haka kuma sai shari'a, shi Almasihu ma, da aka miƙa shi hadaya sau ɗaya tak, domin ya ɗauke zunuban mutane da yawa, zai sāke bayyana, bayyana ta biyu, ba a kan maganar kawar da zunubi ba, sai dai domin yǎ ceci waɗanda suke ɗokin zuwansa.

—Ibraniyawa 9.24-28

IKONSA ZAI KAI MU SAMA A GIDAN ALLAH

"Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto." —Ayyukan Manzanni 4.12

# 38 IKON YESU KRISTI YA ISA YA CECI KOWANI MAI ZUNUBI KOME YAWAN ZUNUBANSA

Maganan nan tabbatacciya ce, ta kuma cancanci a karɓe ta ɗungum cewa, "Almasihu Yesu ya shigo duniya ne domin ceton masu zunubi." —1 Timoti 1.15a

Gama ba na jin kunyar bishara, domin ita ce ikon Allah mai kai kowane mai ba da gaskiya ga samun ceto. —Romawa 1.16a

"Amma duk wanda ya sha ruwan da zan ba shi, ba zai ƙara jin ƙishirwa ba har abada. Ruwan da zan ba shi kuwa zai zama maɓuɓɓuga a gare shi, yana ɓuɓɓugowa har ya zuwa rai madawwami." —Yahaya 4.14

Amma ta alherin da Allah ya yi musu kyauta sun sami kuɓuta ta wurin fansar da Almasihu Yesu ya yi. . . . Yesu Almasihu ya zama hadayar sulhu, ta wurin ba da gaskiya ga jininsa. . . . domin ya nuna adalcinsa ne, . . . ya jingine zunuban da aka gabatar. —Romawa 3.24, 25a

Ku ƙara ba da himma ku tabbatar da kiranku da zaɓenku da aka yi. Domin in kun bi waɗannan halaye, ba za ku fāɗi ba har abada. —2 Bitrus 1.10b

Ga shi, na ba ku ikon . . . ku kuma rinjaye a kan dukan ikon Maƙiyi . . . . —Luka 10.19

# CETO BA ABIN ARHA NE BA, AMMA AN BA MU SHI KYAUTA

## ALLAH YA BIYA TAMANI MAI GIRMA!

"Saboda ƙaunar da Allah ya yi wa duniya har ya ba da makaɗaicin Ɗansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kada ya halaka, sai dai ya sami rai madawwami.

—Yahaya 3.16

## UBANGIJIN DUKAN HALITTA YA MUTU DOMIN DUKANMU

Sai Yesu ya ce, "Ya Uba, ka yi musu gafara, don ba su san abin da suke yi ba." Sai Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Ya Uba, na sa ruhuna a ikonka." Da ya faɗi haka kuwa, ya cika.

—Luka 23.34a da 46

## CETO KYAUTA CE GA DUK WANDA YA KARƁA

Ruhu da amarya suna cewa, "Zo." Duk wanda ya ji kuwa, yă ce, "Zo." Duk mai jin ƙishirwa ya zo, duk mai bukata, yă ɗibi ruwan rai kyauta. —Wahayin Yahaya 22.17

## ALLAH UBAN YA ƘAMNACI AMARYAR ƊAN RAGO (PANSASSU) DAIDAI DA ƊANSA. BABU ƘAMNA WADDA TA FI HAKA GIRMA!

Ni a cikinsu, kai kuma a cikina, domin su zama ɗaya sosai, duniya ta gane kai ne ka aiko ni, ta kuma gane ka ƙaunace su kamar yadda ka ƙaunace ni. —Yahaya 17.23

# KA BA DA KANKA GA YESU KRISTI UBANGIJI YANZU

## KA BAYYANA ZUNUBANKA GA ALLAH, KA YI TUBA

In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukkan rashin adalci. —1 Yahaya 1.9

Wannan kuma ita ce shaidar, cewa Allah yā ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Kansa. Duk wanda ke da Ɗan, yana da rai. Wanda ba shi da Ɗan Allah kuwa, ba shi da rai.
—1 Yahaya 5.11, 12

"Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba za i sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi." —Yahaya 3.36

Ku tuba, ku juyo, domin a shafe zunubanku.
—Ayyukan Manzanni 3.19a

Ba ku sani ba, shi wanda kuke miƙa kanku gare shi domin yi wa biyayya, lalle ku bayi ne na wanda kuke yi wa biyayya ɗin (ko bautar zunubi wanda ƙarshensa mutuwa ne, ko bautar biyayya wadda ƙarshenta adalci ne)? —Romawa 6.16

Kada kuma ku miƙa gaɓoɓinku su zama kayan aikin mugunta don yin zunubi. Amma ku miƙa kanku ga Allah. —Romawa 6.13a

### ƘAMNA MAIMAKON TSORO

Ai, Allah ba halin tsoro ya ba mu ba, hali mai ƙarfi ne, mai ƙauna, da kuma kamunkai.

—2 Timoti 1.7

Ba tsoro ga ƙauna, amma cikakkiyar ƙauna takan yaye tsoro.

—1 Yahaya 4.18a

### ƘAMNA MAIMAKON ƘIYAYYA

Kowa ya ce yana ƙaunar Allah, alhali kuwa yana ƙin ɗan'uwansa, to, maƙaryaci ne. Don wanda ba ya ƙaunar ɗan'uwansa da ya ke gani, ba dama ya ƙaunaci Allah wanda bai ma taɓa gani ba. Wannan kuma shi ne umarnin da muka samu daga gare shi, cewa mai ƙaunar Allah, sai ya ƙaunaci ɗan'uwansa kuma.

—1 Yahaya 4.20, 21

Albarkar Ruhu kuwa ita ce ƙauna. —Galatiyawa 5.22a

### BANGASKIYA MAIMAKON SHAKKA

Wa zai iya raba mu da ƙaunar da Almasihu ke yi mana? Kunci ne? ko masifa? ko tsanani? ko yunwa? ko huntanci? ko hatsari? ko takobi? Duk da haka kuwa a cikin wannan hali duka, har mun wuce ma a ce mana masu nasara, ta wurin wannan da ya ƙaunace mu.

—Romawa 8.35 da 37

Kada halinku ya zama na son kuɗi. Ku dangana da abin da kuke da shi, gama Allah kansa ya ce, "Har abada ba zan bar ka ba. Har abada kuma ba zan yashe ka ba."
—Ibraniyawa 13.5

SALAMA MAIMAKON TSORO

Na bar ku da salama. Salamata nake ba ku. Ba kamar yadda duniya ke bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada kuma ku ji tsoro. —Yahaya 14.27

Kwallafa rai ga al'amuran halin mutuntaka ƙarshensa mutuwa ne, ƙwallafa rai ga al'amuran Ruhu kuwa rai ne da salama.
—Romawa 8.6

To, da ya ke mu kuɓutattu ne ta wurin bangaskiya, muna da salama ke nan a gun Allah ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu.
—Romawa 5.1

WADATA MAI GASKIYA, BA KWAḌAYI

Ya kuma ce musu, "Ku kula fa, ku yi nesa da kowane irin kwaɗayi, don yawan kaya ba shi ne rai ba." —Luka 12.15

Ku saurara, ya 'yan'uwana ƙaunatattu. Ashe, Allah bai zaɓi gajiyayyun duniyan nan su wadata da bangaskiya, har su sami gado cikin mulkin nan da ya yi wa masu ƙaunarsa alkawari ba?
—Yakubu 2.5

TABBATASWA MAIMAKON SHAKKA

Na rubuto muku wannan ne, ku da kuka gaskata da sunan Ɗan Allah, domin ku tabbata kuna da rai madawwami. —1 Yahaya 5.13

TSARKAKEWA, MAIMAKON RASHIN TSABTA

Da ya ke kun tsarkake ranku kuna yi wa gaskiya biyayya har kuna nuna sahihiyar ƙauna ga 'yan'uwa, sai ku himmantu ga ƙaunar juna da zuciya ɗaya. —1 Bitrus 1.22

Alhali kuwa manufar gargaɗinmu ƙauna ce, wadda ke bulbulowa daga tsarkakakkiyar zuciya, da lamiri mai kyau, da kuma sahihiyar bangaskiya. —1 Timoti 1.5

MATUKAR FARINCIKI, MAIMAKON BAƘINCIKI

Allah mai kawo sa zuciya yă cika ku da matuƙar farin ciki da salama saboda bangaskiyarku. —Romawa 15.13a

Na gaya muku haka domin farin cikina ya kasance a cikinku, farin cikinku kuma ya zama cikakke. —Yahaya 15.11

Haka ku ma yanzu kuke tare da baƙin ciki, amma zan sāke ganinku, sa'an nan zuciyarku za ta yi fari, ba kuwa mai ɗauke muku farin cikinku. —Yahaya 16.22

### ĶARFI MAIMAKON RASHIN ĶARFI

A ƙarshe kuma ku ƙarfafa ga Ubangiji, ga ƙarfin ikonsa.

—Afisawa 6.10

### SA ZUCIYA MAIMAKON RASHIN BEGE

Muna sauraron cikar sa zuciyan nan mai albarka, wato bayyanar ɗaukakar Allahnmu Mai Girma, Mai Cetonmu Yesu Almasihu.

—Titus 2.13

Domin albarkacin abubuwa guda biyun nan marasa sākewa, masu nuna, cewa ba shi yiwuwa Allah ya yi ƙarya, mu da muka gudu muka sami mafaka, mu ƙarfafa ƙwarai mu riski abin da muka sa zuciya a kai. Sa zuciyan nan kuwa da muke da ita, kamar anka take ga rai, kafaffiya, tabbatacciya, ita ce kuma ke shiga har can ciki bayan labulen. —Ibraniyawa 6.18, 19

### GASKIYA MAIMAKON RIKICI

Ku yi halin yabo a cikin al'ummai, don duk sa'ad da suke kushenku, wai ku mugaye ne, sai su ga kyawawan ayyukanku, har su ɗaukaka Allah ran da alheri ya sauko musu. —1 Bitrus 2.12

### GASKIYA MAIMAKON ĶARYA

"Za ku san gaskiya, gaskiyar kuwa za ta 'yanta ku."

—Yahaya 8.32

NASARA MAIMAKON KASAWA

Domin duk wanda ke haifaffen Allah yana nasara da duniya. Bangaskiyarmu kuwa ita ce ta sa muka yi nasara da duniya.
—1 Yahaya 5.4

Na kuma ga wadanda suka yi nasara da dabban nan, da siffarta, da kuma lambar sunanta, a tsaitsaye a bakin bahar na gilas, da molayen yabon Allah a hannunsu.
—Wahayin Yahaya 15.2

YIN GIRMA MAIMAKON ZAMAN KAMAR JARIRI

Saboda haka sai mu ci gaba a kan ka'idodin farko na al'amarin Almasihu har ya zuwa kammala, ba wai mu sāke koyar da jigajigan nan na tuba da ibada marar tasiri ba, da na gaskatawa da Allah.
—Ibraniyawa 6.1

Kamar jariri sabon haihuwa, ku yi marmarin shan madara marar gami mai ruhu, domin ku girma da shi, har ya kai ku ga samun ceto.
—1 Bitrus 2.2

Maimakon haka sai mu faɗi gaskiya game da ƙauna, muna girma cikinsa ta kowace hanya, wato Almasihu, shi da yake shugabanmu.
—Afisawa 4.15

### ḲARFAFFAWA CIKIN MUTUM NA CIKI

Ina addu'a ya yi muku baiwa bisa ga yalwar ɗaukakarsa, ku ƙarfafa matuƙa a birnin zuciyarku ta Ruhunsa. —Afisawa 3.16

Zan iya yin kome albarkacin wannan da yake ƙarfafata. —Filibiyawa 4.13

### BA YA DANGANA GA HIKIMAR MUTUM

Jawabina da wa'azina ba su danganta ga maganar rarrashi ko ta wayo ba, sai dai ga rinjaye na ikon Ruhu. —1 Korantiyawa 2.4

### IKON SHAIDA

"Amma za ku sami iko sa'ad da Ruhu Mai Tsarki ya sauko muku, za ku kuma zama shaiduna a Urushalima, da duk ƙasar Yahudiya, da ta Samariya, har ya zuwa iyakar duniya." —Ayyukan Manzanni 1.8

"Mu kuwa shaidu ne ga waɗannan al'amura, haka kuma Ruhu Mai Tsarki, wanda Allah ya bai wa masu yi masa biyayya." —Ayyukan Manzanni 5.32

Manzanni kuma suka yi shaida da tabbatarwa mai ƙarfi kan tashin Ubangiji Yesu daga matattu. Alheri mai yawa na tare da kowannensu. —Ayyukan Manzanni 4.33

# IKON ALLAH SHI KIYAYE MASU GASKANTA GARESHI



Ba na roƙonka ka ɗauke su daga duniya, sai dai ka kare su daga Mugun nan. —Yahaya 17.15

Ta haka salamar Allah, wadda ta fi gaban dukkan fahimta, za ta tsai da zukatanku da tunaninku ga Almasihu Yesu. —Filibiyawa 4.7

Sai ya ce musu, "Na ga Shaiɗan ya faɗo daga sama kamar walƙiya. Ga shi, na ba ku ikon taka macizai da kunamai, ku kuma rinjaye a kan dukan ikon Maƙiyi, ba kuwa abin da zai cuce ku ko kaɗan.

—Luka 10.18, 19

Tun da ya ke ka kiyaye maganar da na yi maka ta yin jimiri, ni ma zan kiyaye ka daga sharrin lokacin nan na gwaji, wanda zai auko wa dukan duniya don a gwada mazaunan duniya.

—Wahayin Yahaya 3.10

Duk wanda ya ci nasara, yake kuma kiyaye aikina har ƙarshe, shi zan bai wa iko a kan al'ummai.

—Wahayin Yahaya 2.26

Ku ƙarfafa ga Ubangiji, ga ƙarfin ikonsa. Ku yi ɗamara da dukan makamai na Allah, don ku iya dage gāba da kissoshin Iblis.

—Afisawa 6.10b, 11

Ku jibga masa dukan taraddadinku, domin yana kula da ku.

—1 Bitrus 5.7

## NAMU TA WURIN BANGASKIYA, ALLAHNMU MAI IKO MARA IYAKA KAḌAI KE IYA CIKAWA

"Kome kuka roƙa da addu'a, in dai kuna da bangaskiya, za ku samu." —Matiyu 21.22

In kun zauna a cikina, maganata kuma ta zauna a cikinku, za ku roƙi duk abin da kuke so, za a kuwa yi muku. —Yahaya 15.7

"Ku yi ta roƙo, za a ba ku. Ku yi ta nema, za ku samu. Ku yi ta ƙwanƙwasawa, za a kuwa buɗe muku. Duk wanda ya roƙa, akan ba shi, mai nema na tare da samu. Wanda ya ƙwanƙwasa kuma za a buɗe masa." —Matiyu 7.7, 8

Wannan ita ce amincewarmu a gabansa, wato in mun roƙi kome bisa ga nufinsa, sai ya saurare mu. In kuwa muka san kome muka roƙa yana sauraronmu, mun tabbata mun sami abin da muka roƙa a gare shi ke nan.

—1 Yahaya 5.14, 15

"Lalle hakika, ina gaya muku, duk wanda ke gaskatawa da ni, ayyukan da nake yi, shi ma haka zai yi. Har ma zai yi ayyukan da suka fi waɗannan, domin zan tafi wurin Uba. Duk abin da kuka roƙa da sunana kuma zan yi, domin a ɗaukaka Uban ta wurin Ɗan. Kome kuke roƙa da sunana, zan yi shi." —Yahaya 14.12-14

Don haka ina dai gaya muku, kome kuka roƙa da addu'a, ku gaskata cewa samamme ne, za ku kuwa samu. —Markus 11.24

Ka nemi farin cikinka a wurin Ubangiji, zai kuwa biya maka bukatarka. Ka miƙa kanka ga Ubangiji, ka dogara gare shi, zai kuwa taimake ka. —Zabura 37.4, 5

Ubangiji kuwa ya ce, "Da kuna da bangaskiya, ko da misalin ƙwayar mastad, da za ku ce wa wannan durumi, 'Ka ciru, ka dasu cikin teku,' sai kuwa ya bi umarninku." —Luka 17.6

Allahna kuma zai biya muku kowace bukatarku daga cikin yalwar ɗaukakarsa da ke ga Almasihu Yesu. —Filibiyawa 4.19

Ya ku ƙaunatattuna, in zuciyarmu ba ta ba mu laifi ba, sai mu je gaban Allah da amincewa. Mukan kuwa sami duk abin da muka roƙa a gare shi, domin muna bin umarninsa, muna kuma yin abin da yake so. —1 Yahaya 3.21, 22

Sai Yesu ya ce masa, "In zan iya? Ai, dukkan abu mai yiwuwa ne ga mai ba da gaskiya." —Markus 9.23

Domin dukan alkawaran Allah cikarsu a gare shi take, ta wurinsa ne kuma muke faɗar "Amin", domin a ɗaukaka Allah. —2 Korantiyawa 1.20

Published in numerous languages by World Missionary Press, Inc., as God supplies funds in answer to prayer. **For questions or more information by country, visit: www.wmp-contacts.org**

Cover photo STScI-PRC2003-11a of Helix Nebula courtesy of NASA and STScI

World Missionary Press
PO Box 120
New Paris, IN 46553-0120 USA
www.wmpress.org

Read booklets online or by App
www.wmp-readonline.org

8-23

736 Haus